**Rahoton Tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu na sayarwa na shekara ta 2012 daga Clive James shugaban kungiyar ISAAA Wannan rahoto sadaukarwace ga mutane sama da miliyan dubudaya dake fama da yunwa a fadin duniya.**

**Tsirran da aka bunkasa kwayar halittarsu sun samu bunkasa kwarai da gaske daga hekta miliyan daya da dubu dari bakwai (milliyan 1.7) a shekara ta 1996 zuwa hekta miliyan dari da saba'in a shekara ta 2012**

An samu cimma hekta miliyan dari da Saba'in da digo uku na tsirrai da aka bunkasawa kwayar halitta a fadin duniya ya zuwa shekara ta 2012 inda a duk shekara ake samun cigaba na kashi Shidda cikin dari wanda yake dai dai da Karin hekta Miliyan Goma da Dubu Dari uku daga hekta Miliyan Dari da Sittin da aka samu a shekara ta 2011.

Shekara ta 2012 hakika shekara ce da aka samu bunkasar tsirran da akan canzawa kwayar halitta ninki-ba-ninki daga hekta Miliyan daya da dubu dari bakwai a shekara ta 1996 zuwa hekta Miliyan dari da Saba'in a shekara ta 2012- hakan shi ya tabbatar da cewa tsirran da aka canzawa kwayar halitta sune suka fi bunkasa a tarihin kwana kwana nan nan

saboda gagarumin cigaban da aka samu tsakanin shekara ta 1996 zuwa ta 2012 , domin miliyoyin manoma ne a kasashen Talatin a fadin duniyar nan suka yankewa kansu hukuncin shuka tsirren da suke da fadin hekta miliyan Dubu daya da miliyan dari biyar, wanda fadin wannan fili ya kai kashi hamsi na fadin kasar China ko Amurka, hakan shi ya jaddada irin yarda da amincin da manoma suka baiwa tsirran da aka canzawa kwayar halitta wanda ke samar da moriya ta bunkasar tattalin arziki da kuma gyara muhalli a fadin duniya.

Sababbin kasashe Biyu ne aka samu a karon farko suka fara amfani da wannan tsari a shekara ta 2012 data gabata kasashen kuwa sune Kasar Sudan (data yi amfani Audigar da aka canzawa kwayar halitta)_sai kasar Cuba ( data shuka Masarar da aka canzawa kwayar halitta). Sai dai kasashen Jamus da Sweden a shekara ta 2012 basu samu damar shuka dankalin turawa ba na "Amflora" a dalilin rashinsa a kasuwarsa, kasar Poland itama ta dai na shuka Masarar da aka canzawa kwayar halitta a dalilin wasu matsaloli na ka'idoji.

Cikin kasashe Ashirin da Takwas da suka noma tsirren da aka canzawa kwayar halitta a shekara ta 2012 Ashirin daga cikin su kasashe ne masu tasowa a inda sauran Takwas din kasashen masu cigaban masa'antu ne, idan aka kwatanta da shekara ta 2011 da cewa kasashe Goma Sha Tara ne masu tasowa Goma kuma masu arzikin masa'antu ne. hakika a shekara ta 2012 an samu bunkasa manoma Miliyan Goma Sha Bakwai da suka shuka tsirren da ka canzawa kwayar halitta watau karin Dubu Dari Shidda ke nan daga shekara ta 2011 kuma kashi Chasa'in cikin dari na manoman watau kimanin manoma miliyan goma sha biyar kananan manoma ne ko masu karamin karfi a kasashe masu tasowa. Manoma sun kware wajen kare samun asara a shekara ta 2012 domin kananan manoma miliya Bakwai ne da Dubu Dari Biyu da kuma karin wasu kananan manoma Miliyan Bakwai da Dubu Dari Biyu a kasar Indiya suka zabi su shuka Audugar da aka canzawa kwayar halitta data kai ta hekta miliyan Sha Biyar saboda moriyar da ake samu.

A karon farko a shekara ta 2012 an samu kasashe masu tasowa sune suka shuka kashi Hamsin da Biyu cikin dari inda kasashe masu cigaban masana'antu suka shuka kashi Arba'in da Takwas cikin dari, bunkasar tsirren da aka canzawa kwayar halitta a wanna shekara ta ninka har sau uku da kuma kara yawa har sau biyar a kasashe masu tasowa watau kashi sha daya cikin dari ko kuma hekta Miliyan Takwas da Dubu dari Bakwai idan a ka kwatanta da kasashe masu cigaban masa'antu da suka samu kashi uku cikin dari watau Karin hekta Miliyan Daya da Dubu dari Shidda. Kasar Brazil a karo na hudu itace kan gaba wajen fadada yawan hektocin noma tsirren da aka canzawa kwayar halitta domin a shekara ta 2012 ta kara yawansu da Miliyan Shidda da Dubu Dari Uku ma'ana an samu Karin kashi Ashirin da Daya daga shekara ta 2011 da yasa yanzu yawan filin nomarta yakai hekta Miliyan Talatin da Shidda da Dubu dari Shidda.

Kasar amurka na cigaba da zama kasa ta kan gaba dake noma hekta miliyan Sittin da tara da Dubu Dari Biyar wadda kuma take noma sama da kashi Chasa'in cikin dari na ire-iren tsirren da aka canzawa kwayar halitta, a shekara ta 2012 kasar Amurka ta samu karancin masara da kashi Ashirin da Daya cikin dari sai kuma waken suya da kashi sha Biyu

cikin Dari, a yayinda kasar Kanada ta samu Nasarar Noma irin Canola daya kai Hekta miliyan Takwas da |Dubu Dari Hudu da nasarar kashi Chasa'in da Bakwai da digo Biyar cikin Dari.

Haka kuma kasar Indiya ta samu nasarar Noma hekta Miliyan Goma da Dubu dari Takwas na Audugar da aka canzawa kwayar halitta da samun nasarar kashi Chasa'in da Uku cikin Dari, kuma kananan manoma Miliyan Bakwai da Dubu Dari Biyu ne a kasar Chaina suka noma Audugar da ta kai hekta miliyan Hudu da samun nasarar kashi Tamanin cikin Dari da kwatan kwacin rabin hekta ga kowane manomi, kasar Indiya ta habbaka kudaden shiga da take samu daga Audugar da aka canzawa kwayar halitta daga Miliyan Dubu Goma sha Biyu da digo Shidda na Dalar Amurka tsakankanin shekara ta 2002 zuwa ta 2011 da Dalar Amurka miliyan dubu Ukku da digo biyu a shekara ta 2011 kadai.

A Nahiyar Afrika ma ana samun cigaba inda Kasar Afrika ta Kudu ta cigaba da fadada filayen da take noma tsirren da aka canzawa kwayar halitta da hekta Dubu dari Shidda da yanzu yawansa ya kai hekta Miliyan Biyu da Dubu Dari Tara, haka kasar Sudan itama ta shiga sahun kasashen Afrika na Afrika Kudu da Burkina faso da Misira inda yanzu kasashen Afrika hudu kenen dake noma tsirren da aka canzawa kwayar halitta a nahiyar.

Kasashen Nahiyar Turai Biyar ne suka Noma hekta Dubu dari da Ashirin da Tara da Saba'in da daya na Masarar da aka canzawa kwayar halitta a shekara ta 2012 watau an samun Karin kashi Goma sha uku daga shekara ta 2011, kasar Sipania itace kan gaba a nahiyar turai da hekta Dubu dari da Goma sha Shidda da dari uku da Bakwai na Masarar da aka canzawa kwayar halitta watau ke nan an samu karin kashi Ashirin cikin Dari ke nan daga shekara ta 2011.

Daga shekara ta 1996 zuwa shekara ta 2011 Tsirran da aka canzawa kwayar halittarsu sun taimaka gaya wajen samar da isashen abinci a fadin duniya da kiyaye muhalli da kuma samar da Karin kayan noman da ya kai na dalar Amurka m Miliyan Dubu Chasa'in da Takwas da digo Biyu dake tallafawa a samun ingantaccen muhalli domin ya hana ayi amfani da maganin Kwari daya kai nauyin kilo miliyan dari Hudu da Saba'in da Uku, a shekara ta 2011 kawai an rage Iskar Gas mai guba ta kabon da ozaid da ya kai yawan nauyin kili Miliyan Dubu Ashirin da Uku da yake kwatan-kwacin hana Motoci sama da Miliyan Goma yawo a tituna haka wannan tsari na amfani da tsirren da aka canzawa kwayar halitta ya taimaka an rage amfani da hekta Miliyan Dari da Takwas da Dubu dari uku na dazuzzuka, sai kuma rage fatara da talauci da tallafawa kananan manoma miliyan Sha Biyar marasa karfi hakan na nufin tallafawa iyalai da suka kai sama da Miliyan Hamsin a fadin duniya.

Hakika tsirren da aka canzawa halitta suna tallafawa sai dai wannan hanya ba itace ingantacciyar tsarin noma ba, dake bukatar sauyi na abin shukawa lokaci zuwa lokaci domin hana kangarewar tsirrai, sai dai har yanzu rashin ka'idojin kimiyya da suka hada da na lokaci da kashe kudade na daya daga cikin kalubalen da wannan tsari ke fuskanta na rashin samun nasara, bugu da kari akwai bukatar ka'idoji kwarara marasa tsauri a kasashe matalauta da kuma masu tasowa domin bunkasar wannan tsari

An kimanta kayayyakin gonar tsirren da aka bunkasa kwayar halittarsu a fadin duniya a shekara ta 2012 da cewa zasu kai Dalar Amurka Miliyan Dubu Goma Sha biyar. Hasashe- Ana sa ran samun bunkasar wannan tsari anan gaba musamman yanda kasashe masu tasowa dama masu arzikin masana'antu suka rungumi wannan tsari da kayayyaki gonar da aka fi bukata a kasuwanni

kungiyar ISAAA daba ta kasuwanci bace wadda Gwamnati da sassa masu zaman kansu ke tallafawa. Duk wani kiyasin hektoci dake cikin rahoton ISAAA sau daya ake gidaya shi, ba tare da la'akari da wadannen irin shuke-shuke ke nan ba. Cikakken bayanai suna nan a ISAAA Brief 44 "Global Status of Commercialized Clive James ne ya wallafa domin Karin bayani sai a ziyarci adireshin yanar Gizo http://www.isaaa.org ko lambar waya +254 20 4223618, ko kuma sakon E mel a africenter@isaaa.org.